# Damawa da masu nakasa a cikin tsarin tazarar haihuwa

Kundin hannu domin **malaman addini**

# Gabatarwa

Yana da muhimmanci masu nakasa su ji a ransu cewa zasu iya yin komai, su samu kwarin guiwa, sannan kuma a karfafa musu gwiwa a lokacin da suke neman yin tsarin tazarar haihuwa. Kuma yana da muhimmanci su san hakkokinsu game da lafiyar bangaren haihuwa.

A wani bangare na shirin damawa da masu nakasa cikin tsarin tazarar haihuwa wato Inclusive Family Planning (IFPLAN) project a turance, kun halarci taron horaswa a kan wayar da kan masu nakasa da shigar da su tsarin tazarar haihuwa hadi da hakkokinsu kan batutuwan da suka shafi jima'i, daukan ciki da haihuwa da reno da kuma tazarar haihuwa.

Bayanan da ke cikin wannan littafin da aka tsara domin malaman addini da shuwagabannin al'umma zai kasance tunatarwa ne kan maudu'an da aka gabatar a lokacin da aka horas da ku.Ya kuma kunshi yadda za'a shigar maudu'an ta hanyar amfani da nassosi daga litattafan addini a cikin wa'azuzzuka da hudubobi, wanda hakan zai ba ku kwarin guiwar yin kira, wa'azi da bayar da shawarwari a kansu.

A matsayinku na shuwagabanni, ana girmamawa da mutunta ku. Sannan an aminta da ku, kuma kuna da tasiri a zukatan mutane. Za ku iya ba da gudunmawa a yankunanku ta hanyar sanar da masu nakasa tsarin tazarar haihuwa da aka tanadar musu da kuma yadda za su samu, sannan kuma su yanke shawara kan tazarar haihuwa tare da abokan zamansu.

Ta hanyar fitowa fili ka kalubalanci karairayi da ake yadawa game da masu nakasa, da kuma bayyana hakkokin masu nakasa game da lafiyar bangaren haihuwa, sannan za ku iya karfafa daukacin al'umarku domin su yi riko da dabi'u masu kyau kan harkar kafiya a kan marassa galihu daga cikinsu.

## Game da shirin IFPLAN

Shirin shigar da ko damawa da masu nakasa tsarin tazarar haihuwa wato IFPLAN, shiri ne da UK Aid ke daukar nauyi bisa jagorancin Sighsavers. Shirin da ake sa ran kammalawa a watan Disambar shekarar 2025, yana samun tallafi daga BBC Media Action, hadakar kungiyar masu nakasa, kungiyar mata masu nakasa, hukumar lafiya a matakin farko ta kasa da ma'aikatar lafiya ta jihar Kaduna.

Shirin na da muradin saukaka samun tsarin tazarar haihuwa ga masu nakasa, musamman ma mata da mata masu karacin shekaru da kuma masu tasowa a jihar Kaduna da ke tarayyar Najeriya. Shirin na fatar kai wa ga mutane masu nakasa da dama ta hanyar amfani mutanen da ke da tasiri a rayuwarsu kamar malaman addini da masu sarautun gargajiya da ke iya shiga cikin al'umomin da ba sa samu ko karbar ingantattun bayanai ko sakonni kan tazarar haihuwa.

Shawara ta zabi na.

Inclusive Futures

UKaid from the British people

# Kunshiya


Gabatarwa 02

Game da shirin IFPLAN 02

Nakasa da kula da lafiyar jima'i 04

Nuna kyama da wariya 04

Karairayi da rashin fahimta 05

Lafiyar mata game da batutuwan da suka shafi jima'i, daukan ciki, haihuwa da reno da kuma hakkokin masu nakasa 06

Kalaman da ake alakanta masu nakasa da shi 07

Tsarin kiran nakasa a farko 08

Tsarin kiran mutum a farko 08

Me ya sa tsarin tazarar haihuwa yake da muhimmanci? 08

Me ye yake hana mutane samun ayyukan tsarin tazarar haihuwa? 09

Isar da sakonnin tazarar haihuwa 10

Tazarar haihuwa a mahangar addinai da litattafai masu tsarki 11

Addinin Kirista 11

Addinin Musulunci 13

Amfani da tasirinka: Maimaici 15

# Nakasa da kula da lafiyar jima'i

Hukumar lafiya ta duniya (WHO) ta yi kiyasin cewa kaso 16 cikin dari na yawan mutanen duniya na rayuwa da wani nau'in nakasa, hakan na nufin mutane kimanin biliyan 1.3 (ko kuma mutun daya cikin mutane shida). An yi kiyasin cewa kusan kaso tamanin na wadannan mutane biliyan 1.3 suna rayuwa ne a kasashe da ke sahun can kasa ko madaidaita wajen samun kudaden shiga, kamar Najeriya. An fi samun nakasa a tattare da mata idan aka kwatanta da maza.

Ana daukar mutane masu nakasa a matsayin wadanda ba'a damu da su ba,inda dabi'u da yanayin zamantakewa ke sa a musu wani irin kallo na daban.Sai dai mata masu nakasa suna da damar samun kulawar lafiyar bangaren haihuwa kamar kowa a cikin al'uma.

Maza da mata masu nakasa suna da hakkin a mutunta jikinsu, a basu damar sirri da cin gashin kansu. Suna da damar yin abubuwa kamar haka:

- Su yanke shawarar lokacin da za su haihu.
- Su zabi abokin mu'amalar ta bangaren jima'i.
- Su yanke shawarar yin aure, lokaci da kuma wanda za su aura.
- Su yanke shawarar ko suna son haihuwa, yaushe za su haihu, da waye suke so su haihu sannan kuma 'ya'ya nawa za su haifa.
- Samun bayanai, kayan aiki, da tallafin da suke bukata domin cimma abubuwan da aka zayyano a sama, ba tare da nuna wariya, tsangwama, tilastawa ko cin zarafi ba.
- Su yi mu'amalar aure mai cike da jin dadi da tsafta ba tare da wata matsala ba.

Hakkoki kan batutuwan da suka shafi jima'i da haihuwa abubuwa ne na bai daya. Sun shafi kowa da kowa. Amma duk da haka mutane masu nakasa na fuskantar wariya a ayyukan kula da lafiyarsu ta bangaren jima'i da haihuwa musamman ma a bangaren neman amincewarsu da basu kariya. Sannan kuma akwai karancin jagoranci da shawarwari musamman idan aka zo bangaren abubuwan da ya kamata jami'an kula da lafiya a bangaren al'amuran jima'i da haihuwa su yi wajen neman amincewa da kare hakkokin masu nakasa. Hakan yana kara taskance mutane masu nakasa daga yin abubuwan da yake hakkinsu ne.

A matsayinku na shuwagabannin al'umma, kuna da wajibcin sanin hakkokin mutane masu nakasa domin tabbatar da cewa ba a bar kowa a baya ba. Akwai bukatar ku gujewa duk wasu ayyuka da ra'ayoyin da basa kulawa ko la'akari da hakkokin masu nakasa.

## Nuna kyama da wariya

Kalmar nuna kyama tana nufin nuna rashin amincewa da mutane da yawa a cikin al'umma ke nuna wa wani mutum saboda wani abu na dabam da yake da shi. Wadannan abubuwa na rashin amincewa da wasu ke gani zai iya zama na abin da ke da alaka da nakasar kwakwalwa, jiki ko wata tawaya a bangaren mu'amala. Hakan rashin adalic ne, kuma kan iya yin illa da kuma nuna wariya wa mutum, ciki har da ware shi/ta daga cikin al'umma.

Ana yawan hana mutane masu nakasa bayanai game da hakkokinsu kan al'amuran da suka shafi lafiyar jima'i da haihuwa, ciki har da hakkin da suke da shi na kulla alaka da yin soyayya, da kuma yanke hukunci kan lokaci da kuma wanda zasu gina iyali da su. Wannan nuna kyama da munanan dabi'u da wariya ka iya zuwa daga iyali, al'umma da ma'aikatan lafiya. Daga cikin nuna kyama da ake yiwa masu nakasa akwai shaci fadin cewa basu da sha'awa, sannan zai yi wahala a ci zarafinsu, sannan nakasa da Allah ya musu ba zai barsu su yi mu'amalar aure ba. Wasu masu nakasa sun fi wasu takwarorinsu fuskantar wariya wajen samun ayyukan kula da lafiyar jima'i da na bangaren haihuwa da suke bukata. Masu nakasar da suka fi fuskantar wariya a wannan bangaren sun hada da masu nakasar gani da nakasar kwakwalwa.

## Karairayi da rashin fahimta

Zamu duba wasu shaci fadi da aka fi samu game da nakasa ta hanyar yin tambaya mai amsar “haka ne ko ba haka ba” da ke da alaka da kundin majalisar dinkin duniya kan hakkonin masu nakasa, wato United Nations Convention on the Rights of Persons with Disabilities (CRPD) a turance.

### Tambaya ta 1

A karkashin kundin CRPD, kowa da kowa (ba tare da la’akari da nau’in nakasarsa/ta ba) na da hakkin zaban ko ya yi/ta yi aure ko kuma ya/ta zauna haka, sannan kuma ya/ta zabi lokaci da wanda ya/take son aura.

Haka ne ko ba haka ba?

### Amsa

**Haka ne!** Karkashin sashi na 23 na kundin CRPD, kowa yana da hakkin kar a tsangwameshi a dukkanin lamura da ke da alaka da aure, iyali, zama iyaye ko soyayya, ciki harda bangaren tazarar haihuwa, lafiyar haihuwa da rayuwar iyali.

### Tambaya ta 2

A kan samu wani yanayi da ma’aikatan lafiya, iyaye da sauran masu kula (bisa tsarin da suka ga ya dace) su dakatar da wasu masu wani nau’in nakasa daga samun ‘ya’ya.

Hakane ko ba haka ba?

### Amsa

**Ba haka ba ne!** Sashi na 23 ya yi bayanin cewa kowa yana da hakkin kada a nuna masa wariya a kowanne lamari da ke da nasaba da aure, iyali, haihuwa da soyayya, ciki har da bangaren tazarar haihuwa, lafiyar haihuwa da rayuwar iyali.

### Tambaya ta 3

Ba kowa ne doka ta baiwa karfin iko na daukar mataki game da lamarin da ya shafi lafiyar bangaren haihuwarsu ba.

Haka ne ko ba haka ba?

### Amsa

**A’a, ba haka ba ne!** Sashi na 12 ya yi bayanin cewa doka ta bai wa kowa karfin iko da hakkin cin gashin kai game da yanke hukunci kan lafiyar bangaren haihuwa.

### Tambaya ta 4

Dole ne masu nakasa su yi amfani da duk irin tsarin kiwon lafiyar da suka samu. Ba dole ba ne wannan tsarin ya dace dari bisa dari da bukatarsu ba, amma hakan ya fi babu, sannan babu wani abu da zasu iya yi a kai.

Hakane ko ba haka ba?

### Amsa

**A’a, ba haka ba ne!** Sassa na 6, 9 da na 25 sun yi bayanin cewa: “kowa yana da hakkin samun kulawar lafiya ciki har da lafiyar al’amuran da suka shafi lafiyar jima’i da haihuwa da ake bayarwa ta hanyar neman amincewa daga wanda za a yi wa aikin da kuma samun bayanai.

# Lafiyar mata game da batutuwan da suka shafi jima'i, daukan ciki, haihuwa da reno da kuma hakkokin masu nakasa

Mutane masu nakasa suna fuskantar wariya a lokacin da suka je neman lafiya game da batutuwan da suka shafi jima'i, daukan ciki,haihuwa da reno. Mafi shahara daga wariya da ake samu shi ne al'umma sun yi amanna cewa masu nakasa basu da sha'awa. Hakan na sa a hanasu bayanai saboda tunanin cewa basa bukatar sanin komai kan lafiyarsu game da batutuwan da suka shafi jima'i, daukan ciki,haihuwa da reno da kuma tazarar haihuwa. Sannan akwai rashin fahimta da yawa da kuma tunanin cewa mutane masu nakasa suna bukatar wata kulawa ce ta musamman.

Mutane masu nakasa har ila yau, suna fuskantar kyama, munanan dabi'u da wariya da kuma rashin girmamawa da rashin daidaito wajen samun kulawa daga ma'aikatan lafiya, al'umma da ma iyalansu. Hakazalika, suna fuskantar rashin amincewa da kuma ba da kariya da ta wuce kima daga iyalansu ciki har da abokan zamansu na aure da masu kula da su kan amfani da tsarin tazarar haihuwa da magungunan hana daukar ciki.

Sannan a wasu lokutan basa samun bayanai kan batutuwan da suka suka shafi lafiyar jima'i, daukan ciki,haihuwa da reno ne saboda rashin kwarin gwiwa da ganin cewa basu kai ba. Mata masu nakasa zasu iya fuskantar cin zarafin jinsi musamman cin zarafi dag makusantansu, wanda hakan ka iya takaita musu samun daman amfani da tsarin tazarar haihuwa.

Mutane masu nakasa za su iya rasa damar zuwa cibiyar lafiya da ke yankunansu saboda rashin hanyar da za su bi a asibitin ko kuma nisan da cibiyar lafiyar ke da shi daga gidajensu, ko kuma rashin iya magana da ma'aikatan da basu samu horaswa kan magana da su ba, kuma ba zasu iya basu bayanai ba.

Mata masu nakasa suna fuskantar nau'ikan wariya dabam dabam kan nakasarsu da kuma jinsinsu. Hasalima, za su iya samun wariya daga maza da mata da basu da nakasa kan nakasar da Allah ya yi musu, yayin da a daya bangaren kuma suke fuskantar wariya saboda jinsinsu da kuma samun kansu da suka yi a cikin al'umar da maza ne kadai ke da katabus.

Akwai karancin ingantattun alkaluma kan batutuwan da suka suka shafi lafiyar jima'i, daukan ciki,haihuwa da reno na masu nakasa. To saidai alkaluma da ake da su sun nuna cewa mutane masu nakasa suna samun mummunan sakamakon lafiya idan aka kwatanta da sauran al'umma.

Rahoton Missing Billion na shekarar 2022 ya samar da maslaha kan yadda za a mayar da tsarin lafiya ta yadda zai samar da dama wa masu nakasa, wanda ya yi bayani kan rashin daidaito game da batutuwan da suka shafi lafiyar jima'i, daukan ciki,haihuwa da reno. Misali:

- Akwai yuwuwar manya da ke da nakasa a yankin Saharar Afirka basa samun bayani kan hanyoyin kariya da kuma yadda cutar HIV ke yaduwa (kimanin kaso 23 cikin dari) idan aka kwatanta da mutane da basu da wata nakasa (kimanin kaso 33 cikin dari).
- Mata masu nakasa sune a sahun baya wajen amfani da tsarin tazarar haihuwa na zamani (kaso 44 cikin dari) idan aka kwatanta da mata da basa da nakasa (kaso 48 cikin dari).

Wani nazari da aka yi kan bincike 29 daga kasashe bakwai yayi nuni da cewa mata masu nakasa suna da yuwuwar kaso 25 cikin dari na samun gwajin kansar mama da kuma kaso 37 cikin dari na gwajin kansar bakin mahaifa idan aka kwatanta da takwarorinsu da basu da wata nakasa.

**Mata masu nakasa suna da bukatar lafiya kamar kowa. Mata masu nakasa suna bukatar samun kula kan lafiyar jima'i, daukan ciki,haihuwa da reno kuma suna da hakkin yin tazarar haihuwa.**

# Kalaman da ake alakanta masu nakasa da shi

Kalaman da muke amfani da su a kan masu nakasa na da muhimmanci. Amfani da kalmomi masu kyau na karfafa masu nakasa, sannan muna nan kalmomi za su iya zama masu ciwo, tayar da hankula da nuna wariya, wanda ke yin mummunan tasiri ga wadanda ake amfani da su akansu. Abubuwan da ke tafe wasu ne daga cikin misala na kyawawan kalmomi da kuma munanan kalmomi da ya kamata a kiyaye su.

| Kalmomin da ya kamata a yi amfani da su | Almomin da basu dace a yi amfani da su ba |
|---|---|
| Mutane masu nakasa/Mutum mai nakasa | Mutane masu bukata ta musamman/ guragu/ matsorata |
| Mutum mai ko mutane masu nakasar (sunan nakasa) | Makaho/ kurma da sauran su |
| Mutanen da basu da nakasa/mutum maras nakasa | Marasa matsala |
| Mai nakasar gani | |
| Mutum mai nakasar kafa/ masu amfani da keken tallafawa zirga-zirga | Masu rayuwa a keken guragu/ masu keken guragu |
| Mai nakasar ji | Kurma, makaho, maras ji |
| Gajeren mutum/ mai nakasar girma | Wada |
| Mutum mai nakusar fahimta/karatu | Maras hankali, mahaukaci, mai tabin hankali/kwakwalwa |
| Mutum mai nakasar kwakwalwa | Maras tunani/ wawa/ mahaukaci |
| Mutum mai lalurar cuta mai tsanani | |

## Tsarin kiran nakasa a farko

Wasu masu nakasa sun fi son tsarin saka nakasarsu a farko idan za a yi magana da su, misali, a matsayinka/ki na mai fama da nakasa. Wasu sun fi son bayyana kansu da sunaye kamar mai nakasar gani, ko nakasar ji da sauransu.

## Tsarin kiran mutum a farko

Wasu kuma sun fi son tsarin kiran sunan mutum a farko kafin nakasar da suke fama da ita idan za su gabatar da kansu misali, mutum mai nakasar gani, mutum da wayau da tunaninsa yake kasa da shekarunsa.

**Idan ka hadu da mai nakasa a farko, ka tambayesu kalmomin da suka fi so ayi musu amfani da su.**

# Me ya sa tsarin tazarar haihuwa yake da muhimmanci?

Tsarin tazarar haihuwa bai sabawa kowanne addini ba, sannan bai karfafa gwiwar matasa da marassa aure su yi watsi da tarbiya ba. Hasalima, tsari ne da ya dace saboda dalilai da yawa: Wadannan dalilai sun hada da:

- Yana ba da kariya daga hatsarin lafiya da ke da alaka da shayarwa wanda ake yaye yaro a dole ba tare da ya girma ba saboda daukar wani ciki.
- Yana kare uwa daga hatsarin lafiya saboda daukar ciki akai akai ba tare da tazara ba ko kuma a karancin shekaru.
- Yana rage yawaitar mutuwar mata masu juna biyu.
- Yana taimaka wa iyaye su gujewa wahalhalun tattalin arziki sakamakon kulawa da iyalai masu yawan gaske, wanda ka iya tursasa musu fadawa haramtattun ayyuka ko kuma yin ayyukan da suka fi karfinsu.
- Yana rage yawan haihuwar yara a cikin al'umma, wanda hakan ke takaita haihuwa a cikin al'ummomin da yawansu ke karuwa. Hakan na shafar samun gidaje, ayyukan yi, ilimi da abinci.
- Yana ba da dama wa yaro ya samu ingantaccen ilimi, wanda an fi samunsa idan yara basu da yawa.
- Wasu daga cikin nau'ikan da ake amfani da su na tazarar haihuwa na kare yaduwar cututtukan da ke ake samu ta hanyar jima'i ciki har da cutar HIV.

Mafi yawan malaman addini ba tare da la'akari da addini ko kungiyarsu ba, sun yi ittifakin cewa dukkanin iyalai sun cancanci su yi rayuwa mai inganci ba tare da shan wata wahala ba. To sai dai mafi yawan iyalai basa samun damar hakan saboda rashin tsarin tazarar iyali, rashin ilimi kan tsarin da ake da shi, ko kuma rashin samun damar kaiwa gare su.

Idan wa'azuzzuka da hudubobi suka mayar da hankali wajen magance matsalolin zai taimaki mata da iyalai da dama wajen samun tsarin tazarar haihuwa, sannan su tsara yawan 'ya'yan da za su haifa tare da kwarin guiwa da tabbaci kan kulawa da su.

# Me ye yake hana mutane samun ayyukan tsarin tazarar haihuwa?

Akwai dalilai da yawa da ke hana mutane masu nakasa samun damar kai wa ga tsarin tazarar haihuwa. Wadannan abubuwa sun hada da:

"Ba na tunanin akwai **tsarin tazarar haihuwa na kyauta ko kuma cibiyoyin tsarin tazarar haihuwa** a kusa da ni."

"Mutane a cikin al'ummar da nake sun yi imanin cewa **mutane masu nakasa ba za su yi aure su haihu ba**."

"Iyalaina suna da fahimtar cewa tsarin tazarar haihuwa an tanadar wa **masu aure ne kadai**."

"Ina bukatar **amincewar mijina** domin amfani da tsarin tazarar haihuwa."

"Mutanen da ke cikin al'ummata suna da fahimtar cewa kada na yi amfani da tsarin tazarar haihuwa **saboda fahimtar addini**."

# Isar da sakonnin tazarar haihuwa

Shigo da harkar tazarar haihuwa a cikin wa'azuzzuka da hudubobi na hada al'umma waje guda karkashin imani da kulawa da lafiya. Yana bayani kan alfanun da tazarar haihuwa ke da shi a rayuwar al'umma baki daya, kama daga iyaye, lafiyar yara zuwa ga kudaden shiga na iyali, gidaje da ilimi. Wa'azinku da hudubarku za su iya wayar da kan al'uma, su kasance masu fahimta da kuma sanya ido kan lamuran da ke da alaka da tazarar haihuwa ta yadda za su saukaka hakan wa mutane da yawa, da kuma kore labaran kanzon kurege. Za a iya isar da sakon a wajaje dabam dabam, a cibiyoyin ibada ko kuma wajajen bukukuwan addini ko wajajen tarurrukan al'uma mabambamta.

A kowanne tsarin addini ko al'uma kake, sakonnin da ke kasa na da muhimmanci ka shigo da su cikin wa'azuzzuka da hudubobinka ko ma sauran jawabai.

---

**Yana da muhimmanci a fahimci cewa kalmar wa'azi ko huduba ana amfani da su ne domin bayyana wani jawabi da malaman addini ke gabatarwa a lokacin ibada, taro ko wani biki. Mafi yawan wa'azuzzuka da hudubobi suna mayar da hankali ne kan amfani da labarai daga cikin litattafai masu tsarki domin ayi koyi da darussan da ke ciki, to amma wa'azi ko huduba zai iya nufin karantawar addini kan abubuwan da suka shafi al'uma. Zaka iya samun karantawar addini da ya goyi bayan tazarar haihuwa (karkashin addinin Musulunci da Kiristanci) daga shafi na 11 zuwa gaba.**

---

**Akwai nauyin da ya rataya a wuyanku a matsayin shuwagabannin al'uma na ilmantar da su kan tazarar haihuwa.** Aiki ne da ya rataya a wuyanku ku ilmantar da mutane masu nakasa da ke al'umarku kan adadi da kuma lokacin da ya kamata ku dauki ciki. Su nemi a samar musu da bayanai hadi da kayan aikin tazarar haihuwa wa kowa da kowa a cikin al'umma, ba tare da la'akari da nakasarsu ba.

**A karfafa shigar da maza.** Sakon a mafi yawan lokuta yafi mayar da hankali kan yara mata da manyan mata, ta yadda yara maza da manyan maza ake barinsu a baya, domin ba a karfafa musu guiwa su shigo a dama da su wajen yanke hukunci kan tazarar haihuwa, kai a wasu lokutan har nuna musu kyama ake yi idan suka yi hakan.

**A kalubalanci rashin daidaito.** Wasu dalilai da suka hada da ilimi, yanayin tattalin arziki ko karfin jiki yana nufin mutane da dama basa samun bayanai kan tazarar haihuwa. Dukkanin addinai an ginasu ne akan daidaito da adalci ga marassa galihu, da kuma yin hidima ga mabukata. Dole ne a bada dama wa mutane masu nakasa da ke cikin al'umarka kamar kowa.

**Ayi amfani da damarmakin hadin gwiwa.** Wajajen taron addini da na al'uma na bada damar haduwar mutane da ke da mabambamtan shekaru, kwarewa da karfi. Ku yi amfani da wannan farfajiya wajen isar da ilimin tazarar haihuwa da kalubalantar karairayi da rashin fahimta game da nakasa da haihuwar yara, sannan a karfafa hadaka tsakanin mutane daga dukkanin fajjojin rayuwa. Ku gayyaci jami'an kiwon lafiya domin su yi jawabi wa al'umarku a wajen tarurrukansu kan tazarar haihuwa, wadanda zasu bada gamsassun bayanai kan tazarar haihuwa.

# Tazarar haihuwa a mahangar addinai da litattafai masu tsarki

## Addinin Kirista

A karkashin karantarwar addinin Kirista, Allah ne ya halicci wajen hada alakar saduwa kamar yadda yake (A littafin Farawa sura ta 1 aya ta 27c ) sai kuma magana akan alaka da jin dadi sannan kuma an yi magana akan hayayyafa (a littafin Farawa sura ta 2 aya a 18, 25).

A addinin Kirista ubangiji ya lura da rayuwar mutum tun daga ciki. Kowanne rai yana da muhimmanci kuma Allah ya tsara masa yadda zai rayu. Allah ya tsarawa kowanne mutum yadda zai rayu, ciki harda zai ji dadin duniya m A don haka yana da kyau a gina iyali yadda ya kamata.

Tsarin hana daukar ciki na zamani ba su samu ba a lokacin saukar da littafin mai tsarki l, a don haka littafi bai ce komai ba game da shi. Littafin injina ya bayyana 'ya'ya a matsayin kyauta daga Allah (kamar yadda yake a littafinFarawa sura ta 4 aya ta 1, da Farawa sura ta 33 aya ta 5. Sannan kuma gado daga Allah kamar yadda yake a (littafin zabura, sura ta 127, aya 3-5), albarka daga Allah kamar yadda yake a (littafin Luka sura ta 1 aya ta 42) sannan kambun mulki ga tsofaffi kamar yadda yake a (littafin MISALAI sura ta 17 aya ta 6). A don haka tsara haihuwa, tsawon kwana da ingancin rayuwar yara babban aiki ne akan iyaye.

Tsarin tazarar haihuwa ta hanyar hana daukar ciki da Ilimi kan lafiyar haihuwa hanya ce ta tsara rayuwa aure ta yadda zai tabbatar da cewa an hana shigar ciki a lokacin da aka tabbatar zai amfani uwa, dan da zata haifa da kuma iyali. Ba hanya ba ce ta amfani da tazarar iyali da zai jawo tambayoyi kamar yadda yake a labarin Onan da ke cikin littafin Injila (Farawa sura ta 3 aya ta 8), saidai hanya ce ta yin wani abu da zai jawo tamabaya kan abin da ya kamata.

Wasu ma'aurata na ganin cewa aikin ibadarsu wa Allah da kuma ayyukansu a cikin al'uma ya tursasa musu yin adduo'i a tsaneka kafin yanke hukunci kan yaushe zasu dauki ciki. Wasu sun yi imanin vewa Allah ya tsara musu rayuwa da bai kunshi samun haihuwa ba ko kuma tsarin da ya kunshi samun yara da zarar aj yi aure. To saidai aniyar ma'aurata kan zabin kin haihuwa, jinkirta haihuwa, amfani da tsarin hana daukar ciki ko tara 'ya'ya da yawa ya danganta ne da soyayyarsu ga Allah, soyayyarsu ga makwabtansu (ciki harda wadanda ba a haifa ba) da kuma soyayyar da suke yiwa kansu.

A cewar littafi mai tsarki, 'ya'ya kyauta ne daga Allah, kuma mutum yana kasancewa cikin farin ciki idan yana da 'ya'ya da yawa (Zabura, sura ta 127 aya ta 5. To sai dai a zahiri ba kowa ne yake da damar tara 'ya'ya ba (wato karfin ikon bayar da kulawa wa iyalai da yawa). Idan ma'aurata suka yanke shawarar amfani da tsarin tazarar haihuwa, yana da kyau su yi nazari kan tsarin da yafi dacewa da bukatar iyalinsu.

A karantawar addinin kirista kuwa, tazarar haihuwa ba laifi ba ne matukar za mu nemi yardar Allah a kan abin da za mu yi. James sura ta 4 aya ta 15-17 ya dace da hakan: "Sai ka ce idan Allah ya kaddara za mu kasance cikin rayayyu, mu yi abu kaza da kaza.' To amma sai mutum ya yi tunkaho da girman kai. Dukkanin wannan girman kan aikin Shaidan ne. A don haka, duk wanda yasan abu mai kyau amma ya ki yi to ya aikata zunubi."

(Farawa sura ta 1 aya ta 28) Allah ya ce ga namiji da mace "kasance mai hayayyafa ku yi yawa". Wasu na fassara hakan da cewa kuskure ne a hana daukar ciki da gangan. Amma ainihin ma'anar wannan ayar na nuni ne da yadda Allah ya bai wa dan Adam damar sarrafa duniya, sannan maganar ba akan hana daukar ciki ba ne.

Kuma Allah ya albarkace su, sai Allah ya ce musu, ku hayayyafa ku yi yawa, sannan ku cika duniya, ku amfana da ita, sannan ku jagoranci duk halittu, kama daga kifin da ke ruwa zuwa tsuntsun da ke sama da ma dukkanin halittar da ke rayuwa a bayan kasa." (Farawa 1: 28).

Littafi mai tsarki na mabiya addinin Kirista da sauran karantarwar addinin sun ba da jagoranci da bayanai kan maudu'ai daban-daban da ke da alaka da ibada da tarbiyya, amma bai fito fili ya yi bayani a kan tazarar haihuwa ba. Abin da ya bayyana shi ne wani tsari da zai fahimtar fa mabiya kan tazarar haihuwa ta hanyar yin bayani kan asali da darajar rayuwar dan Adam.

Kamar yadda aka fada a sama Allah ya halicci dan Adam (maza da mata) a halitta ta musamman. Sai kuma ya girmama rayuwar dan Adam ta hanyar sanya hoton kansa a jikin Yesu Almasihu a matsayin mutum kuma yayi alkawarin sake tashinsa a karshen duniya. A duk haka ya kamata a girmama kowanne dan Adam a matsayin kyauta daga Allah.

An yi bayani kan muhimmancin dan sa ba'a kai ga haifansa ba a littafin zabura sura ta139 inda Dauda ya rubuta cewa, "Kai ne ka halicci jikina, ka hada ni waje guda a cikin mahaifiyata, na kasance cikakken mutum, idonka yana kaina tun kafin cikar halittana. A cikin kittafinka yana rubuce kan kwanakina, a lokacin da babu wani da ya wanzu sai kai kadai." (Zabura sura ta 139, aya ta 13-14, 16

Tun a cikin mahaifa a farkon rayuwa, Allah ya yi magana kan rayuwar dan Adam (duba littafin Farawa sura ta 20 aya ta 18, sura ta 22 aya ta 31, sura ta 30 aya ta 2, sura ta 30 aya ta 22, littafin kubawar sharia sura ta 13 aya ta 2-3; Littafin Ruth Sura ta 4 aya 13, sura ta 1, littafin Sama'ila sura ta 1 aya ta 6, littafin Jarmiya sura ta 1 aya ta 5; littafin Luka sura ta 1 aya ta 13-15 da sura ta 1, aya ta 24-25, sura ta 1 aya ta 44. Kyakkyawan tsari da daukar mataki kan daukar ciki da haihuwar yara dole ne ya kasance a sahun gaba a rayuwar gidaje da al'umomin dukkanin mabiya.

**A takaice, muhimman sakonnin tazarar haihuwa a addinin kirista su ne wadanda zasu taimaki daidaikun mutane, iyalai da al'uma domin su yi abubuwa kamar haka:**

- Gudanar da nauyin da Allah ya daura musu na hayayyafa.
- Haihuwar dan da ake so kuma aka shirya masa ta hanyar kaucewa daukar cikin da ba a shirya masa ba.
- Yanke hukuncin kan yawan 'ya'yan da za a haifa kuma a haifesu a lokacin da ya kamata.

# Addinin Musulunci

A Addinin Musulunci, Alkur'ani da hadisan manzon Allah su ne ginshiki wajen karantarwa da shiryarwa kan tazarar haihuwa. An amince da daukar matakan wucin gadi na hana haihuwa, amma matakan din-din-din kam ana amincewa da su ne kadai idan rayuwar matar na fuskantar barazana.

Jawabi ga Limamai: A karanta dukkanin ayoyin da aka kawo cikin harshen larabci har karshe kafin a fassara zuwa turanci ko kuma wani yare na dabam.

## Jagoranci/bayanai daga Alkur'ani Maigirma

Alkur'ani bai haramta amfani da tsarin hana daukar ciki ba, kuma bai hana miji ko mata bayar da tazara ko takaita daukar ciki ba. A don haka mafi yawan Malaman Musulunci sun tafi akan halarci tazarar haihuwa a addinin Musulunci.

Alkur'ani ya fito fili ya bada shawarar iyaye mata su shayar da 'ya'yansu na tsawon shekaru biyu cikakku: Kamar yadda Allah ya ce; "kuma iyaye mata su shayar da 'ya'yansu na tsawon shekaru biyu..." (Alkur'ani sura ta 2 aya ta 233).

A cikin Alkur'ani, an kira shayar da nonon uwa zalla sau 14 a matsayin hanyar tazarar haihuwa, hakan ke nuna cewa Alkur'ani ya goyi bayan shayar da nono a matsayin hanyar tazarar haihuwa. Sannan akwai ittifaki tsakanin malamai kan wata ayar Alkur'ani da ta bayyana cewa a bada tazara tsakanin yara. Iyaye mata su shayar da 'ya'yansu nono na tsawon shekaru biyu, inda a lokacin mace ba zata dauki ciki ba.

**Allah ya ce a cikin Alkur'ani:**

"Iyaye mata su baiwa 'ya'yansu na tsawon shekaru biyu cikakku, ga wadanda ke da muradin cika lokacin (Alkur'ani sura ta 2 aya ta 233).

Sai muka yi wasiyya wa mutum da ya kyautata (yayi biyayya) wa iyayensa. Mahaifiyara ta dauke shi cikin gazawa da wahala, sannan ta yaye shi cikin shekaru biyu." (Alkur'ani sura ta 31 ayq ta 14).

Malamai sun bayyana wadannan shekaru biyu na shayarwa a matsayin hanyar tazarar haihuwa domin baiwa iyaye mata wadataccen lokaci su huta daga daukar cikida haihuwa sannan su kula da dan da suka haifa. Wadannan shekaru biyu na shayarwa sun dace da shawarar shayarwa na hukumar lafiya ta duniya WHO.

Wani shiryarwa daga Alkur'ani shi ne kan tsarin ubangiji na halittar abokan zaman da ikonsa domin abokan zaman su samu daidaito da zaman lafiya karkashin inuwa guda. A cikin suratul Rum sura ta 30 aya ta 21 inda Allah ya ce: Yana daga cikin ayoyinsa, ya halicceta muku abokan zama daga kawunansu domin ku samu nutsuwa da ita, sannan ya saka soyayya da tausayi a tsakaninku.

Hakan na nufin cewa ana so ma'aurata sundinga tattaunawa da juna kan tsarin tazarar haihuwa kafin yin amfani da shi. Ana hakan ne domin tabbatar da zaman lafiya da kula da lafiyar gida da daidaito tsakanin ma'aurata.

## Jagoranci/bayanai daga Hadisi (Maganganun manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi)

Sunnah ita ce abubuwan da aka tattaro na maganganu da ayyukan manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi, wanda ya tabbata cewa tsarin nan na janyewa wato Azalu an yi shi a lokacin Manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi.

**Jagoranci/bayanai na 1 daga Hadisi**

"Sahabbban manzon Allah mun kasance muna yi azalu a lokacin manzon Allah kuma ya sani amma bai haramta ba." (Sahih Muslim, littafi na 16, hadisi mai lamba 161 -163).

Sunnar bata yi magana akan tazarar haihuwa kai tsaye ba, amma tayi magana akan hadda Manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi yasan sahabbbansa suna yin azalu kuma lokacin da ya samu labari bai haramta aikatawa ba. A don haka mabiyansa suka yi amanna cewa in da ace an haramta yin hakan a Musulunci to babu makawa da ya hana su kai tsaye. Makasudin yin azalu shi ne hana shigar ciki kamar dai tsarin hana daukar ciki na wucin gadi a zamanance.

Tunda dai an amince da yun tsarin tazarar haihuwa ta hanyar shayar da nono da kuma azalu, musulmai na da damar neman bayanai da shawarwari kan ayyukan tazarar haihuwa. Yana da kyau a bayar da bayanai masu muhimmanci wa ma'aurata da daidaikun mutane (musamman kafin aure) omin basu damar daukar matakin da ya dace da addininsu da kuma lafiyarsu.

**Jagoranci/bayanai na 2 daga Hadisi**

A cikin wani Hadisi da Imamul Bukhari ya fitar, manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi ya ce: "Daga cikin hakkokin da akan iyayensa shi ne su koya masa rubutu, iyo da harbi sannan su samar masa da lafiyayyen abinci (Sahihul Bukhari, Juzu'i na 2 littafi na 22 hadisi mai kamba na 69, an karbo hadisin daga Sahl bin Sa'ad).

Ya kamata a samarwa matasa maza da mata cikakken bayani kan tazarar haihuwa da tsarin tazarar haihuwa hadi da alfanunsa, saboda su dauki matsaya a lokacin da ya dace idan sun yi aure wanda hakan ne zai basu damar kulawa da 'ya'yansu.

**Jagoranci/bayanai na 3 daga Hadisi**

A cikin hadisin da Imam Ahmad ibn Hambal ya inganta manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi ya ce ka umarci 'ya'yanka da yin sallah a shekaru bakwai, ka hukunta su idan suka ki yin sallah a shekaru goma, sannan ka raba musu wajen kwanciya." (Musnad na Imam Ahmad, Juzu'i na 2, Hadisi mai lamba na 467, wanda aka karbo daga Abdullahi bin Amr)

Wannana hadisin yana nuna bukatar tsarin haihuwa. Raba wajen kwana na nufin dakin maza dabam da na mata. Bada tazarar haihuwa da kuma yawan iyali da ya dace da karfin samun iyalin na daga cikin maslaha da kuma kulawa da tsarin gidan da iyalin ke rayuwa a ciki.

**Jagoranci/bayanai na 4 daga Hadisi**

A daya daga cikin hadisan da Abdullahi bn Umar ya ruwaito a cikin mustadrak, manzon Allah tsira da amincin Allah su kara tabbata a gareshi ya ce "... babban ganganci ne haihuwar 'ya'ya da yawa ga wanda baya da halin kulawa da su..." (Sahihul Bukhari, Juzu'i na 5, littafi na 64 hadisi mai lamba na 196).

A wani hadisin ya ce 'ya'ya da yawa na iya jawo talauci, 'ya'ya kalilan na kawo rayuwar jin dadi." (Musnad na Imamu Ahmad, Juzu'i na 2, Hadisi mai lamba 5359, Abdullahi bin Umar ne ya ruwaito)

Bayanin hadisin shi ne, karfin al'umar Musulmi ya danganta ne da samun lafiyayyun 'ya'ya masu tarbiyya da suka samu ilimi kuma zasu iya kulawa da kansu a gana kuma su kasance masu amfani wa al'uma - wannan hakan ne ya kawo tsari mai kyau.

### Kammalawa

Acewar mafiya yawan malaman addini, mummunar fassara wa karantarwar addinin Musulunci kan hana daukar ciki ka iya rage karbar tsarin tazarar haihuwa. Karancin ilimi alan bangaren lafiyar haihuwa, munanan al'adu da kuma rashin karfin mata wajen yanke hukunci zai ci gaba da zmaa dalilin kin karbar tsarin tazarar haihuwa a cikin wasu al'umomin musulmi.

Yaki da munanan fahimta kan amfani da tsarin tazarar haihuwa na bukatar shigowar shugabanni da Malaman addini ln Musulunci wanda ke da karfin fada aji da tasiri a matakin al'uma.

Babban sakon tazarar haihuwa a addinin Musulunci shi ne bada tazarar haihuwa yadda ya kamata a iyaki hanya ce mai muhimmanci wajen kare lafiyar iyaye mata da yaran da suke haifa.

# Amfani da tasirinka: Maimaici

A matsayinka na shugaba ko malamin addini a cikin al'uma, an yarda da kai kuma ana girmama ka. Kana da tasiri da hanyar da zaka kai ga al'umar da basa karba ko samun sakonni da bayanai kan tazarar haihuwa.

Ga wasu shawarwari kan yadda zaka taimaka.

- ✓ A shigo da maudu'in takarar haihuwa a cikin wa'azuzzuka da hudubobinka, kamar yadda aka zayyana a sama. Ka duba shafi na takwas kan dalilai daga litattafan addini da nuna goyon baya wa tsarin tazarar haihuwa (na addinin Kirista da Musulunci) wadanda zasu iya maka amfani.
- ✓ Ka karfafawa ma'aurata gwiwa kan tattaunawa da juna da kuma yanke hukunci tare. Ka jagoranci tattaunawar ma'aurata da taron horaswa, ta yadda ma'aikacin lafiya zai hakarta domin masa tambayoyi da kuma bayar da bayanai.
- ✓ Ka tabbatar ka san cibiyoyin kiwon lafiya a yankinka da masu nakasa ke samun damar zuwa, da kuma ayyukan da suke yi. Ka samu bayanai da ake bukata domin taimakawa mutanen da ke rayuwa a cikin al'umarku wadanda ke bukatar bayanai kan waje da kuma yadda zasu samu tsarin tazarar haihuwa.
- ✓ Ku tura mutane masu nakasa zuwa ga jami'in kiwon lafiya da ke cikin al'umarsu idan suna bukatar cikakken bayani ko kuma sun fi son yin magana da su kai tsaye.
- ✓ Ka kasance a fili ta yadda kowa zai yi saukin samunka, ka kasance mai karbar jama'a, mai hakuri, kar ka kasance mai yankewa mutum hukunci a lokacin da mutanen al'umarka suka tunkareka domin tattaunawa kan tazarar iyali.
- ✓ Ka bar hanyoyin sadarwa a bude, sannan ka sanar da al'uma cewa kullum kofarka a bude take domin tattaunawa.

Shawara ta zabi na.

Inclusive Futures

UKaid from the British people